© Beate Frenzel, Gülşah Mavruk (2018)

# Jagorar tattaunawa don tattaunawar farko da ɗalibai ‘ya’yan ‘yan gudun hijira sababbin isowa

## Bayanin jerin tambayoyin

### (Hausa – Übersetzung durch externen Anbieter)

An shirya wannan jerin tambayoyi ne na yanzu a zaman wani jagoran tattaunawa da kuma bayar da muhimmin bayani don musanyar bayani tsakanin malamai waɗanda suke gudanar da tattaunawar samun gurbin karatu ga ‘ya’ya da kuma matasa na ‘yan gudun hijira sababbin isowa (kafin shiga makaranta a ƙasar Jamus).

Dangane da wannan tattaunawar samun gurbin karatu, ya kamata a sani cewa yana aiki ne a matsayin gabatarwar farko ko aikin ƙungiya kuma cewa ba duk tambayoyin da hukumar makaranta take da sha’awa za a warware su nan-da-nan ba. Tambayoyin da ba za a iya amsa su tun da fari ba yawanci sun fi haɗa da batutuwa kamar waɗanda suka shafi iyali da tsira da kuma matsayin zama, saboda wannan zai iya jawo tunanin abin da ya wuce musamman ga yaran da suka firgita. Bugu da ƙari, batutuwa na sha’anin kuɗi waɗanda suka shafi samun rangwamen sa’o’i ko neman ma’aunan BuT (ilimi kan abin da suka shafi kuɗi da kuma shiga ma’aunan JobCenter) za a miƙa su ne kawai idan an ƙulla amintacciyar dangantaka tsakanin malamai da ɗalibai da iyaye da mai riƙe da da yaro ko masu kulawa da yaro da kuma masu kula da walwalar makaranta.

Dole ne a shirya da kuma sajar da ɗaiɗaikun sassa na jerin tambayoyin bisa dacewa da shekara da kuma dabarun harshe na ɗaliban (na gaba). Ba kowace tambaya ce ta dace da

kowane yaro ko matashi ba. Ya rage ga malamin (mai masaukin) ya yanke shawar a kan wannan.

Jerin tambayoyin ya bi muhimmiyar dabara ta gabatarwa. Haka kuma, za a adana duk babarun magana da harshe na yaran. A Sashe na III (Yanayin magana da harshe a cikin ƙasar haihuwa) za a bincika yanki-takamaimai da ake amfani da harshe. Za a iya la'akari da duk wasu ƙananan dabaru (magana da karatu da rubutu da sauraro).

Baya ga wannan jerin tambayoyi, ana bincika bayanin duk makaranta, wuraren koyon sana'a da kuma duk abubuwan sha'awa da gwaninta a cikin harsunan uwa daban-daban na 'ya'yan 'yan gudun hijira sababbin isowa. Wannan yana bayar rarraba rukunoni na masu koyo ba bisa la'akari kawai ga matakin ƙwarewar harshe na yanzu ba, har da dalili da kuma dama ta waɗanda abun ya shafa.

Hukumar gundumar Cologne za ta nazarci duk wasu shahadodi da aka zo da su daga ƙasashen haihuwa don yiwuwar amincewa a zaman shahadar kammala karatun firamare har zuwa shahadar kammala karatun ƙaramar sakandare.
(http://www.bezreg-koeln.nrw.de/brk_internet/leistungen/abteilung04/48/anerkennung/auslaendische_schulzeugnisse/index.html)
Bisa bambanci, hukumar gundumar Düsseldorf ita take da alhaki na amincewa da ɗaukacin takardun karatu na samun damar shiga jami'a.
(http://www.brd.nrw.de/schule/schulrecht_schulverwaltung/Zeugnisanerkennung.html)

Za ka sami wani jerin adabi mai sharhi tare littattafan rubutu da kuma ƙarin kayayyaki na darasi don 'ya'yan 'yan gudun hijira da sababbin zuwa a kan shafin yanar gizo na ProDaZ website https://www.uni-due.de/prodaz/.